# Nagartacciyar Rayuwar Aure

Abubakar Abbas



# Nagartacciyar Rayuwar Aure

**NA**


## Abubakar Abbas

**Hotoro/ Tsamiyar Boka Bus Stop**

**Kano- Nijeriya**

**GSM: 08035945930**

Hafifiin Mallaka (MH):

Abubakar Abbas,

Hotoro/ Tsamiyar Boka Bus Stop

Kusa da Kukar Dillalai.

An fara bugawa a shekarar 2008

An sake bugawa a shekarar 2012

Ba a yarda a yi amfani da wannan littafi ko a sarrafa shi ta kowace irin hanya ba, sai an sami izini daga marubucinsa.

Tsara rubutu da Kwamfuta:

Shehu Ahmad Tudun Wuzirci,

07032509942, 0809549797991, 08153980195.

**GABATARWA**

Godiya ta tabbata ga Allah wanda ya shar'anta aure, kuma ya sanya shi sunnar Manzanninsa.

Tsira da aminci su tabbata ga fiyayyen halitta, Annabi Muhammad (Sallallahu Alaihi Wassallam)wanda yace***"Idan bawa yayi aure ya cika rabin addininsa, sai kuma yaji tsoron Allah a sauran rabin daya rage masa"***. Ɗabarani ne ya rawaito shi. Kuma an karɓo shi ne daga Anas Allah ya yarda da shi.

Bayan haka, kasancewa rayuwar aure a musulunce ta ginu ne akan wasu hafifiofii(nauye-nauye), da sai an kiyaye su take inganta kuma ta kyautata, naga ya dace in rubuta wannan littafi mai suna: Nagartacciyar Rayuwar Aure don fayyace wa 'yan uwa Musulmai hafifiofiin zamantakewar aure, saboda a sami sauyi daga matsalolin da suke addabar ma'aurata Musulmai a rayuwarsu ta aure.

A karshe, ina fatan Allah ya karɓa min wannan aiki, kuma ya saka min da gidan rahamarsa. Sannan kuma ya amfani 'yan uwana Musulmai da wannan littafi, amin.

Abubakar Abbas Ibrahim

Hotoro/ Tsamiyar Boka Bus Stop

Kano-Nijeriya.

**ABUBUWAN DA KE CIKI**

Ma'anar Aure: - - - -

Abubuwan da sai dasu aure yake zama karɓaɓɓe

Cikakken bayani a kansu - - - -

Amfanin samar da shaidu a aure - -

Ranar haɗuwar ango da amarya - -

Nauye –nauyen rayuwar aure - -

Hafifiofiin mace akan miji - - -

(a) Sadaki - - - - -
(b) Ɗora iyali a kan bin Allah tare rainonta da kyawawan ɗabi'u - - -
(c) Samawa mace wajen mazauni - -
(d) Ciyarwa da tufatarwa - - -
(e) Haɗarin fiuntata wa iyali wajen ciyarwa
(f) Dokokin suturar Musulma - -
(g) Ba ta izinin fita yayin bufiata - -
(h) Adalci a zamantakewar miji da matarsa.

## MA’ANAR AURE

Aure wani haɗi ne da ake yinsa tsakanin namiji da matar data halatta da aure agare shi, bayan amincewarsu da juna, domin tabbatar da halaccin gudanar cuɗanya a tsakaninsu da kuma biya wa junansu bufiatar sha’awa ba tare da ansami wani zargi ba.

**Abubuwan Da Saida Su Aure Yake Zama Karɓaɓɓe:**

A musulunce aure na tabbata ne da tabbatar waɗannan abubuwa masu zuwa kamar haka:

1. Samuwar amincewar waɗanda za a ɗaurawa aure.
2. Waliyyin matar da za a aura.
3. Shaidu.
4. Sadaki.
5. Siga. (wato maganganun da aure yake dauruwa da su), kamar mai neman yace da waliyyin mace: ‘Ina neman auren wance’. Sai shi kuma waliyyin yace: ‘Na aura maka ita.

**CIKAKKEN BAYANINABUBUWAN DA SAI**

**DASU AURE YAKE ZAMA KARƁAƁƁE**

**(1) Samuwar Amincewar Waɗanda za a Ɗaura wa Aure**

A shari'ance, aure baya zama zartacce, abin la akari da shi, sai idan an sami yardar ma'aurata da kuma amincewarsu.

Dalili kuwa faɗar Allah Madaukakin: "Ku auri abinda ya kwanta muku a rai daga matan (da suka halatta a gare ku), biyu-biyu ko uku-uku ko kuma hudu-hudu.

Da kuma hadisin da aka karɓo daga Ukbatu ɗan Amir (Allah ya yarda da shi) yace "Hafiifia Annabi ( Tsira da amincin Allah su tabbata agare shi ) yace: "Da wani wani mutum (da zai ɗaurawa aure ) ka yarda in aura maka wance? Sai yace: eh (nayarda), sannan Annabi yace da matar: kin yarda in aura miki wane? Sai ta ce: eh (nayarda), Sai Annabi (tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi) ya ɗaura musu aure". ( Baihafii da Hakim da wasunsu ne suka rawaito shi ).

Kuma Abdullahi ɗan Abbas ( Allah ya yarda da shi ) yace: "Hafiifia, wata budurwa tazo wajen Annabi ( Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ) tace: Babanta ya ɗaura mata aure ( Da wani ) ba da sonta ba ( nan take) sai Annabi ( Tsira da amincin Allah su tabbata agare shi ) ya bata zaɓin idan ta amince da wanda aka aura mata auren ya ɗauru, idan kuma bata son sa, to auren bai ɗauru ba". ( Ahmad da Abu Dawud da wasunsu ne suka rawaito shi).

Sannan an karɓo daga khansa'u 'yar khidan ( Allah ya yarda da ita ) Cewa: Babanta ya ɗaura mata aure da wani tana bazawara ba da sonta ba,sai taje ta shaidawa Annabi ( Tsira da amincin Allah su tabbata agare shi ) sai yace : "Auren bai ɗauru ba". ( Bukhari ne ya rawaito shi ).

**(2)** Waliyyin Matar da za a Aura

Waliyyi shi ne mutumin da alhakin aurar da mace yake wuyansu, kamar uba, ko madadinsa, ko shugaban musulmai.

Waliyyi ma sharadi ne daga sharuddan da sai dasu aure yake dauruwa a musulunce.

Saboda haka, bai halatta mace ta aurar da mace ba, kamar yadda bai halatta mace tayi gaban kanta ta aurar da kanta ga wani ba.

An karbo daga Abu Huraira ( Allah ya yarda da shi ) ya ce: "Manzon Allah ( tsira da amincin Allah su tabbata agare shi ) ya ce : "Mace bata aurar da mace, haka kuma mace bata aurar da kanta". ( Ibn Majah ne ya rawaito shi ).

Kuma an karbo daga Ikrima da Abdullahi ɗan Abbas (Allah yayarda da su) sun ce: "Manzon Allah (tsira da amincin Allah su tabbata agare shi) yace: " Babu aure saida waliyyi".

Sannan kuma an karbo daga Aisha ( Allah ya yarda da ita ) tace: Manzon Allah (Tsira da amincin Allah su tabbata agare shi ) yace: " Duk matar da tayi aure bada izinin waliyyinta ba, auren ɓatacce ne,. Idan kuma wanda ya aure ta akan hakan, har ya sadu da ita to, ya bata sadakinta, saboda saduwar da yayi da ita. Idan kuwa mace da waliyyinta suka saɓa, to, shugaban musulmai shi ne waliyyin duk wacce ba ta da waliyyi". ( Abu Dawuda da Ibn Majah ne suka rawaito shi).

**(3)** Shaidu:

Su kuwa shaidu su ne adalan mutanen da suke halartar gurin ɗaurin aure, su kuma kasance a gurin a lokacin daza a ɗaura auren.

A musulunce, mutane biyu sune mafi fiarancin shidu game da ɗaurin aure. Saboda hadisin da aka karɓo daga Imran ɗan Husaini, da Aisha ( Allah ya yarda dasu ) cewa, Annabi (tsira da

amincin Allah su tabbata agare shi) yace: “ Babu aure sai da waliyyi da kuma shidu biyu adalai”. ( Imam Ahmad ne ya rawaito shi ).

Amfanin Samarda Shidu a Aure:

Yana daga cikin amfanin da samar da shidu yake da shi:

1. Kawar da zargin zina, ko daduro tsakanin ma’aurata.
2. Hana a kira ‘ya’yan da mutum ya Haifa ‘ya’yan zina (shegu).

**(4)** Sadaki:

Sadaki shi ne dukiyar aure, wacce mace take cancantarsa daga wajen miji ta dalilin aure. Saboda faɗar Allah Maɗaukaki:

“kubawa mata sadakinsu cikin daɗin rai, idan kuma suka sayar muku da wani abu daga cikinsa da sonsu (don kansu), to, kuci shi (halak malak ) rai kwance”.

Da kuma faɗar Allah maɗaukaki:“ To, waɗanda kuka ji daɗi da su daga cikinsu (mata) ku basu sadakinsu (cikakke) tilas”.

Sanan kuma Allah da hikimarsa da ya yi bayinsa bai yi su bai ɗaya ba, don haka ma, daya wajabta musu bayar da sadaki, sai ba iyakance musu shi ba. Saboda ya dace da mai hali da kuma mai fiaramin fiarfi. Kowanne gwargwadon halinsa.

Don haka, a musulunce ya halatta mutumin da yake da hali ya dunkule wasu mafiudan kuɗi ya bayar a matsayin sadakin matar da zai aura. Allah Madaukaki yace : “ Idan kuka yi nufin musanya wata mace a maimakon wata (da kuka saka) alhali kuwa da kun bawa dayarsu ( ta farkon ) dukiya mai ɗimbin yawa (a matsayin sadakinta ), to , kada ku karbi komai daga cikinsa, shin kwa karbe shi don zalunci da saɓo mabayyani”.

Sai dai kuma mafi falalar sadaki shi ne wanda bayayinsa ya zo kamar haka:

An karɓo daga Ukbatu ɗan Amir (Allah ya yarda da shi) yace: Manzon Allah (Tsira da amincin Allah su tabbata agare shi) “ya aura wa wani mutum mace akan sadakin zobe na fiarfe”. (Hakim ne yarawaito shi).

Bayan haka kuma, shi sadaki hafifii ne na matar da aka aura, kamar dai yadda bayani ya gabata. Saboda haka, bai halatta ba ga waninta yaci wani abu daga cikin sa, sai dai inda izininta.

To bayan kammalar bayanin waɗannan abubuwa da muka ji, anaso a lokacin daza a gudanar da ɗaurin aure a kwaikwayi Annabi ( Tsira da amincin Allah su tabbata agare shi ) a rigayi ɗaurin auren da gabatar da wannan addu’ar kamar haka:

An karbo daga Abdullahi ɗan Mas’ud ( Allah yayarda dashi ) Yace: Manzon Allah (Tsira da amincin Allah su tabbata agare shi ) ya koya mana yin “ Huɗubar Haja “ a lokacin ɗauren aure. Wato:

Innal hamdulillahi ta’ala, nahmadhu wanastagiynuhu, wanastagfiruhu, wa na’u’zu billahi min shuruwri anfusina wa min sayyi’a’ti a’a’malina, man yahdihil-llahu fala mudilla-lahu, waman yudlil fala hadiyaya lahu, wa’ashadu an lailahaillallahu wahdahu la shariyka lahu, wa’ashadu anna muhammadan abduhuwarasuluhu.

Ya ayyuhal lazina a’manuttafiuwllaha hafifia tufiatuhi wala tamutunna illa wa antum muslimun (Al-i-mran, aya ta (102)

Ya ayyuhannasu-ttafiuw rabbakumullazhiy kalafiakum min nafsin wahida wakalafia minha zaujaha wabassa minhuma rajalan kasiran wa nisa’a’wattafiuwllahal lazhiy tasa’a’luna bihi wal’arhama innallaha kana alaikum rafiiyba (An nisa’i aya (1)

Ya ayyuhal-lazhina ‘a’manuttafiuw-llaha wa fiulu fiaulan sadhidhan yuslih lakum a’a’malakum wa yagfir lakum zhunubakum waman yuɗi’illaha wa rasuluhu fafiad faza fauzan a’zhima (Al Ahzab aya,
Abu Dawud, da Nisa’i da wasunsu ne suka rawaito shi

Sannan kuma ya halatta bayan gama daura aure, ranar akai amarya gidan miji, a buga dundufa domin sanar da aure da kuma faranta ran ango. Amma bai halatta ayi raw aba.

**Ranar Haɗuwar Ango Da Amarya:**

A musulunce ana so ranar da ango ya fara haɗuwa da amaryasa ko kuma ranar da aka kawowa ango matarsa gidansa, yayi fiofiarin yin waɗannan abubuwa masu zuwa kamar haka:

(1) Ango ya jagoranci matarsa suyi Sallah raka’a biyu- nafila don mifia godiyarsa ga Allah daya cika musu burinsu kamar yadda Ibn Abi Shaiba ya rawaito.

(2) Ya ɗora hannunsa akan goshin matarsa, wato yakaanta ya rifie, sannan kuma ya karanta wannan addu’a kamar haka:
“ Ya Allah ina rofionka alherin wannan mata da alherin da ka halicceta akansa, kuma ina neman tsarinka daga sharrinta da sharrin abin daka halicceta akansa”. ( Bukhari a cikin littafinsa da Abu Dawuda da Ibn Majah da wasunsu ne suka rawaito shi ).

(3) Gabatarwa da amarya wani ɗan abin kusa da baka, kamar yadda Annabi (Tsira da amincin Allah su tabbata agare shi ) yayi wa matarsa Aisha (Allah ya yarda da ita ).

(4) Goge baki kafin kwantawa da amarya, domin kawar da wani hamami, ko wari da ka iya tashi daga cikin baki. Kamar yadda aka samu Muslim da Abu Awana sun rawaito Annabi (Tsira da amincin Allah su tabbata agare shi ) ya yi haka.

(5) Yin addu’ar saduwa da mace, kafin fara saduwa da ita. Addu’ar kuwa itace: “ Ya Allah ka nesantani daga shaiɗan ka kuma nesanta shidan daga abin daka azurta ni da shi”.
Annabi ( Tsira da amincin Allah su tabbata agare shi ) yace: Idan Allah ya hukunta wa miji da matarsa samun ɗa a saduwar da suka karanta wannan addu’ar, to, shaiɗan ba zai cutar da ɗan da suka samu ba har abada”. (Bukhari da Muslim da wasunsu ne suka rawaito shi ).

(6) Yin walima da abin da Allah ya hore, bayan tarewa da saduwa da amarya. Saboda aiwatarwar Annabi da kuma umarnin da yayi na ayi walima.
Sannan kuma idan za a kira jama’a walima, to ayi kokarin ganin an tara wadanda suke mabukata, saboda Annabi (tsira da amincin Allah su tabbata agare shi ) yana cewa: “ Mafi sharrin abinci walima, wanda ake kiran (ko gayyatar) mawadata a kyale mabukata “. ( wato a ki gayyatarsu ). ( Malik da Bukhari da Muslim da wasunsu ne suka rawaito shi ).
Daga lokacin da Allah ya hukunta wa Musulmi aurar wata mace, ko kuma ya hukuntawa Musulma auren wani Musulmi, to ya zamar musu lallai su san cewa, a musulunce akwai wasu nauye-nauye da suke tattare da rayuwar da zasu fuskanta ta zaman aure, wadanda suka sha bamban dana irin rayuwar da suka faro a baya ta zaman kaɗaici.

**Nauye-nauyen Rayuwar Aure**:

A musulunce, rayuwar aure bata kyautatuwa ta zama nagartacciya har sai idan an aiwatar da ita ta salon da Musulunci ya tsara, ta hanyar ɗorawa ma’aurata wasu nauye-nauye da ake bufiatarsu dasu sauke su kamar haka:

1. Hafifiofiin mace akan mijinta.
2. Hafifiofiin miji akan matarsa.
3. Hafifiofiin da miji da mata suke tarayya a kansu.
4. Hafifiin wanda mutuwa ta raba shi da abokin zamansa daga cikin ma'aurata.
   1. Hafifiofiin Mace a Kan Mijinta:
      (a) Sadaki: Wanda bayaninsa ya riga ya gabata.
      (b) Ɗora iyali akan bin Allah tare da rainonta da kyawawan ɗabi'u.
      Shi wannan hafifii na biyu da samuwarsa da kuma ɗorewarsa ne mace zata kyautata tsakaninta da ubangijinta, da kuma tsakaninta da bayisa.

Da farko Allah Mai girma da Buwaya yace:

" ka ambaci (labarin) Isma'il cikin wannan littafi (Alfiur'ani), hafiifia shi mai cika alfiawari ne, kuma Annabi ne Manzo. Ya zamanto yana umartar iyalinsa da (tsaida sallah da kuma ba da zakka, sannan kuma shi yardajje ne a wajen ubangijinsa ).

Abin nufi a nan, Annabi Isma'il yardajjen Allah, a zamansa da iyalinsa yana umartar su ne da su rifia tsayar da sallah, kuma su rifia bayar da zakka, domin alafiarsu da Ubangiji ta kyautata.

Sannan kuma munji cewa shi mutum ne mai cika alfiawari, sanin kowa ne kuma duk wanda yake haka zaka tarar yana fiofiarin rainon iyalinsa da yin haka.

Sannan kuma Allah ya ce da Annabi Muhammad (tsira da amincin Allah su tabbata agare shi):

"ka umarci iyalinka da tsaida Sallah kai ma kuma kayi hafiurin dawwama akan tsaida ita, ba zamu tambaye ka dukiya ba, mune ma zamu azurta ka, kuma kyakkyawan fiarshe (duniya da lahira ) ga masu tsoron Allah yake".

Annabi (tsira da amincin Allah su tabbata agare shi ) ya aiwatar da wannan umarni da Allah yayi masa kamar yadda Imamut- Tirmizi ya rawaito hadisi cewa, an karɓo daga Ummu- salama Allah ya yarda da ita tace: " Annabi (tsira da amincin Allah su tabbata agare shi) ya kasance idan watan Ramadan ya rage kwana goma ya fiare, baya barin ko da mutum ɗaya daga cikin mutanen gidansa matukar dai zai iya yin sallar dare face sai ya tashe shi (domin ya yi)".

To, 'yan uwa, idan Annabi bai bar sallar nafila ta wuce mutanen gidansa ba; ina kuma ga sallar farilla.

Sannan kuma Allah Maɗaukaki yace: "yaku waɗanda kuka bada gaskiya, ku tserar da kanku da kuma iyalanku (daga shiga ) wuta (wadda ) mutane da duwatsune makamashinta, kuma akwai wasu karfafan mala'iku masu kauri da suke tsaron ta, waɗanda basa saɓawa Allah abin daya umarcesu da shi, kuma suna aikata duk abin da aka umarce su da shi".

A wannan ayar kuma kiran muminai gaba ɗaya Allah ya yi, sannan ya umarce su dasu dage su bi irin turbar da Annabawa suka bi, wajen ɗora kansu da iyalansu akan hanyar bin Allah da nisantar saɓa masa, domin su gudu tare su kuma tsira tare.

Har wa yau, Bukhari ya rawaito hadisi da aka karɓo shi daga Malik ɗan Huwairis Allah ya yarda da shi yace: Annabi (tsira da amincin Allah su tabbata agare shi) yace da (ayarin) jama'ar Abdul- Kais da

suka zo wajen “su kiyaye imaninsu da kuma ilimin ɗaya sanar dasu shi, sannan kuma yace dasu, “ku koma wajen iyalanku ku sanar da su”.

Saboda waɗannan dalilan da muka ji ya zama lallai akan miji ya sanar da matarsa ilimin yadda zata bautawa ubangijinta, ko kuma ya turata inda zataje ta koya, kamar yadda matan sahabbai suke zuwa wajen Annabi (tsira da amincin Allah su tabbata agare shi ) su koyo addini.

Bayan haka, an karɓo daga Amru ɗan Ahwas Allah ya yarda da shi yace, ya ji Annabi (tsira da amincin Allah su tabbata agare shi ) a hajjinsa ta bankwana yana cewa: “ku saurara, kuyiwa mata wasici da alheri”. ( Tirmizi ne ya rawaito shi ).

Haka kuma an karɓo daga Aisha (Allah ya yarda ita ) ta ce: “ (wata rana ) Yahudawa sun zo wajen Annabi (tsira da amincin Allah su tabbata agare shi) sai suka ce dashi: “Assamu alaikum” wato halaka ta tabbata akanku, a maimakon su ce: “Assalamu alaikum” wato amincin ya tabbata agare ku, jin haka, sai Aisha ta ce: Halaka akanku, Allah kuma ya tsine muku; yayi fushi daku. Sai Annabi yace da ita: ‘A’a Aisha, yi a hankali, ina umartarki da yin saufii, kuma ki kiyayi kausasawa da munanan maganganu. Sai kuwa tace da Annabi baka ji abin da sukace ba ne? Annabi yace: To ke bakiji abin dana ce dasu ba? Ai na mayar musu da martani da cewa a kansu dai. Sai Allah ya amsa mini addu’ar dana yi musu, su kuma ba zai amsa musu wadda suka yi mini ba. (Bukhari ya rawaito shi).

A nan idan muka lura da kyau, za mu fahimci cewa, waɗannan hadisai suna ɗora magidanta ne akan hanyar daya kamata su ɗora matansu akai, ta nusar dasu yadda ya kamata su zauna da mutane a cuɗanyarsu dasu. Allah dai yaba mu ikon kulawa da kuma aiki da wannan koyarwar ta Annabi (tsira da amincin Allah su tabbata agare shi), amin.

**(c) Samawa Mace Mazauni (Gida ko ɗaki):**

Shi kuma wannan nauyi ya hau kan miji ne a sakamakon faɗar Allah Madaukaki daya ce:

“ku zaunar dasu (mata) a inda kuke zaune daidai halinku, kada ku cuce su don ku fiuntata musu”.

Da kuma faɗar Allah Maɗaukaki cewa: “ kuji tsoron Allah Ubangijinku kada ku fitar dasu daga dakunansu, suma kada su fita, sai dai idan sun zo da mummunan aiki mabayyani, waɗancan iyakokin Allah ne, to hafiifia ya cuci kansa”.

Saboda haka, haramun ne mai gida yace da matarsa ta fice tabar masa gidansa,ko ɗakinta don ya saketa, matufiar dai bata gama idda ba. Haka kuma itama mace bai halatta ta bar gidan mijinta ba don ya sake ta har sai bayan ta gama idda. Wannan sai ya tabbatar mana da cewa aihakin miji ne ya tanadar wa matarsa mazauni.

**(d) Ciyarwa da Tufatarwa:**

Haka ma ciyarwa da tufatarwa, hakki ne da mace take da shi akan mijinta. Saboda faɗar Allah Maɗaukaki yace:

“ ciyar da mata da tufatar dasu gwargwadon iko, wajibi ne akan wanda aka haifawa da, ba a ɗorawa (kowanne) rai sai gwargwadon ikonsa”. A wata ayar kuma Allah Maɗaukaki yace: “ Mai yalwa ya ciyar daga yalwarsa, wanda kuma aka fiuntata arzikinsa, (wato talaka), to, ya ciyar daga ɗan abinda Allah yaba shi, Allah baya ɗorawa kowacce rai sai abinda ya bata, da sannu Allah zai sanya saufii bayan matsi (tsanani)”.

A hadisance kuwa, an karɓo daga Hakim ɗan Mu'awiya daga babansa (Allah ya yarda da shi) yace: " Na tambayi Manzon Allah (tsira da amincin Allah su tabbata agare shi) cewa, menene hafifiin matar kowannenmu akansa? Sai yace: " Ka ciyar da ita idan kaci, ka kuma tufatar da ita idan ka tufata...". ( Ahmad da Abu Dawud da wasunsu ne suka rawaito shi).

Sannan kuma sahabin Annabi Amru ɗan Ahwas ( Allah ya yarda da shi ) yace: Hafiifia yaji Annabi (tsira da amincin Allah su tabbata agare shi) a hajjinsa ta bankwana yana cewa: " ku saurara, hakika matanku nada hafifii a kanku, hafifiinsu a kanku ku kyautata tufatar dasu, da ciyar dasu".( Tirmizi ne ya rawaito).

Bisa dogaro da waɗannan dalilai, ya zama tilas akan miji ya ciyar da matarsa, ya tufatar ita gwargwadon irin halin da yake da shi.

Sannan kuma amana ce a wuyan miji ya ciyar da matarsa da halal bada haram ba.

**Haɗarin Kuntatawa Iyali Wajen Ciyarwa**

Musulmin da Allah yayi masa yalwar abin da zai ciyar da iyalinsa, da abin da zai tufatar dasu,amma sai ya zama yana fiuntatamusu, ta hanyar fiin wadata su da abin da zai ishe su, to, a zahirin gaskiya babu wanda yake cuta sai kansa, domin kuwa Annabi (tsira da amincin Allah su tabbata agare shi) yace: "ya ishi mutumlaifi, ya rika tozarta wanda yake ci a fiarfiashinsa". (Abu Dawuda ne ya rawaito shi).

Kuma an karɓo daga Abu Huraira (Allah ya yarda da shi) yace: Hafiifia, Annabi (tsira da amincin Allah su tabbata agare shi) Yace: "Babu ranar da bayi zasu wayi gari a cikinta face sai wasu mala'iku biyu sun sauko, sai ɗaya daga cikinsu ya kama cewa: "Ya Allah ka bai wa mai ciyarwa". Sai shi kuma ɗayan yace: "Ya Allah ka haɗa matsolo da asara". (Bukhari da Muslimu ne suka rawaito shi). Don haka, 'yan uwa sai ayi hattara.

Bayan haka, da Allah zai datar da iyalan malam matsolo da samun wata kafa dazasu rifia ɗiban abin da zai ishesu daga cikin dukiyarsa, a shari'ance, basuyi laifi ba in sun ɗebi abin da zai ishesu, matufiar dai baza suyi ɓarna ba.

An karbo daga Aisha (Allah ya yarda da ita) tace: "Hindu 'yar Utba matar Abi Sufyanu ta shiga wajen Manzon Allah (tsira da amincin Allah su tabbata agare shi) sai tace: " Ya manzon Allah mijina Abu Sufyan matsolo mutum ne, baya bani abin ciyarwa da zai isheni, kuma ya ishi 'ya'yana, sai in na ɗebi wani abu daga cikin kudinsa bada saninsaba, shin ko ina da laifi game da hakan da nake yi? Sai Annabi yace: "kici gaba da ɗaukar abin da zai ishe ki ya ishi 'ya'yanku daga kuɗinsa". Wato yin hakan ba laifi bane. (Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi).

Sannan dai ita wannan ta'ada ta matsolanci, haɗarinta yana da yawan gaske, domin kuwa tana sa mai yinta ya rasa samun alherin da masu ɗaukar abin hannunsu su bayar suke samu:

**Na Farko**: zai rasa samun addu'ar alherin da mala'ika yake yi wa masu ɗaukar abin hannunsu su bayar duk wayewar garin Allah, kamar yadda mukaji.

**Na Biyu**: Ya rasa kwarjinin da masu bayar da abin hannunsu suke samu a wajen waɗanda suke agazawa.

**Na Uku**: An karɓo daga Abu Huraira (Allah yayarda da shi) yace, Manzon Allah (tsira da amincin Allah su tabbata agare shi) yace: "Hannun da yake bayarwa yafi hannun da yake karɓa. (In zaka bayar) ka fara da wanda nauyinsa ke kanka, kaba wa babarka, da babanka, da 'yan uwanka, sannan wanda yafi kusa da

kai, sai wanda yake da kusanci da kai". (Nasa'i da Darakudni ne suka rawaito shi, kuma Darakudni da ibn Hibban suka inganta shi).

**DOKOKIN SUTURAR MUSULMA**

Amana ce akan miji duk suturar da zai yi wa matarsa ta zama daga halaliyar abin da yake da shi. Sannan kuma kada ya kuskura yayiwa matarsa sutura data sha bamban da wadda musulunci ya yarda musulma tasa. Don haka:

(1) Haramun ne miji ya sayowa matarsa koya dinkawa mata irin kayan kafirai. An karbo daga Abdullahi ɗan Amru ɗan Ass ya ce, Manzon Allah (tsira da amincin Allah su tabbata agare shi) ya ganni sanye da wasu kaya biyu masu ruwan ɗorawa, sai yace: "Hafiifia, waɗannan kayan suna daga cikin irin kayan kafirai, kada ka fiara sasu". (Muslim da Nasa'i da Hakim da wasunsu ne suka rawaito shi).
Kuma Abu Dawud ya rawaito hadisi da aka karɓo daga Abdullahi ɗan Umar (Allah ya yarda shi) yace, Manzon Allah (tsira da amincin Allah su tabbata agare shi) yace: "Wanda ya kwaikwayi wasu mutane ya zama ɗan cikinsu".

(2) Haramun ne miji ya sayowa koya ɗinka wa matarsa kayan maza. Saboda hadisin da Abu Dawud da wasunsu suka rawaito cewa, Manzon Allah (tsira da amincin Allah su tabbata agare shi) ya tsinewa mutumin da yake sa kayan mata, haka kuma ya tsinewa matar da take sa kayan maza.

(3) Baya halatta miji ya sayawa ko ya ɗinkawa matarsa kayan neman suna, saboda Annabi (tsira da amincin Allah su tabbata agare shi) yace: "Wanda ya sanya kayan shuhura (neman suna) a duniya, Allah zai sanya masa tufafin fiasfianci ranar alkiyama, sannan kuma Allah ya balbala shi a wuta". (Abu Dawud ne ya rawaito shi daga Abdullahi ɗan Umar( Allah ya yarda dasu).

Tufar neman suna, ita ce tufar da aka yi ta domin yin fice da kuma son zama daban cikin mutane, imma dai ta zama mafi wulafiantar tufa da in aka sata za a jawo hankalin mutane, ko dai da sunan gudun duniya, ko son yin daban da sauran mutane.

(4) Haramun ne miji yabawa matarsa damar sa matsattsun tufafi masu kama jikinta, su kuma siffatashi, ballantana kumashi ya sayo mata matsattsun ko ya ɗinka mata su. Saboda hadisin da aka karɓo daga Usamatu ɗan zaid (Allah ya yarda da shi) cewa, Annabi (tsira da amincin Allah su tabbata agare shi) yana tsoron mace ta sanya tufar da zata rifia siffata kasusuwan jikinta. (Diya'ul Maksidi ne ya rawaito shi).

(5) Sannan dai kuma bai halatta miji ya sayawa matarsa suturar da take shara-shara ba, saboda faɗar Annabi (tsira da amincin Allah su tabbata agare shi) cewa: "A fiarshen Al'umma ta za a samu wasu mata da zasu zama sanye da tufa, amma kuma suna tsirara, kansu kuwa kamar tozon rakumi (In kun gansu ) ku tsine musu, tsinannu ne su". A wani hadisin ya fiara da cewa: Baza su shiga Aljanna ba, kuma baza suji fianshinta ba, ga shi kuwa hafiifia ana iya jiyo fianshinta daga tafiya mai nisan kaza da kaza". (wato mai nisan gaske ). (Ɗabarani ne ya rawaito shi).

(6) Lallai ne miji ya tabbatar cewa, suturar da zai yiwa matarsa, ta zama wadda zata rufe mata baki ɗayan jikinta.

**(e) Bata Izinin Fita Yayin Buƙata:**

Yana daga cikin hafifiofiin da mace take da su akan miji, yaba ta izinin fita domin zuwa ta biya bufiatar data same ta, wadda bata saɓawa shari'a ba, kamar zuwa gaisuwar mutuwa, ko duba mara lafiya, ko jajantawa wani Musulmi da wata musiba data same shi, ko sada zumuntar 'yan'uwa da dai sauransu.

Bukhari da Muslim da wasunsu ne suka rawaito shi daga Aisha (Allah ya yarda da ita) wanda a cikinsa Annabi (tsira da amincin Allah sutabbata agare shi) Yace: "Allah yabawa mata damar fita domin biyan bufiatunsu". Amma fa kuma lallai ne miji ya kula wajen ganin matarsa tabi fia'idojin da Musulunci ya shimfiɗawa mata; a yayin fita unguwa, kamar rashin cin ado da sanya turare, bin gefen hanya, rashin ɗaga murya da shewa akan hanya, da dai sauran su.

An karɓo daga Abi Masal Ash'ari (Allah ya yarda da shi) yace, Manzon Allah (tsira da amincin Allah su tabbata agare shi) yace: "Duk matar da ta sa turare ta kuma gifta wasu mutane domin suji fianshinta, to ita karuwa ce". (Nisa'I da wasunsu ne suka rawaito shi).

Sannan kuma baya halatta mabayyaniyar suturar mace ta zama mai ado caɓa-caɓa, a yayin da zata fita unguwa, saboda faɗar Allah Maɗaukaki: "Ku mata ku tabbata cikin ɗakunanku, (ko gidajenku) kada ku bayyanar da adonku irin bayyanar da ado (lokacin maguzancin farko)".

Kuma Manzon Allah (tsira da amincin Allah su tabbata agare shi) yaceda Umaimatu 'yar Rufiaika a lokacin data yi caffar karɓar Musulunci: "Zan yi caffa dake akan… ba zaki bayyanar da adonki ba, irin bayyanar da adon (lokacin) maguzancin farko". (Ɗabarani ne ya rawaito shi daga Abdullahi ɗan Abbas Allah ya yarda da shi).

Bayan haka kuma, bai kamata mace ta rifia tashin hankalin kanta dana mijinta ba, a daliln ta nemi izinin fita a wajensa bai barta ba, a nan hafiuri shi ne mafi dacewar abin daya kamata mace tayi, sannan kuma ta tuna faɗar Allah Maɗaukaki: "Ba komai da kuke so kuke samu ba, sai Allah ya so".

(f) Adalci, a zamantakewar miji da matarsa:

Adalci, shi ne yin abu bisa cancanta da kamala.

Hafifiin mace ne akan miji ya rifia yin hulɗa da ita bisa cancanta da kamala, a cikin maganganunsa da ayyukansa, kamar irin yadda yake son matarsa ta yi hulɗa da shi bisa cancanta da kamala (wato ya zauna da ita batare da ya nuna sakaci ko zalunci ba, musamman idan mai auren fiye da mace ɗaya ne).

An karbo daga Abdullahi ɗan Amr ɗan Ass, Allah ya yarda da su yace: Manzon Allah (tsira da amincin Allah su tabbata agare shi) yace: "Dukkan wanda ke son a nesanta shi daga wuta, kuma a shigar da shi Aljanna, sannan mutuwarsa tazo masa yana mai ba da gaskiya da Allah da ranar lahira, to ya rinfia yiwa mutane irin abin da yake so suyi masa". (Muslim ne ya rawaito shi).

Kuma an karɓo daga Aisha (Allah ya yarda da ita) tace: "Manzon Allah (tsira da Amincin Allah su tabbata agare shi) ya kasance baya fifita wasunmu akan wasu wajen raba mana kwana da zaman da yake yi a wajenmu….". (Abu Dawud ne ya rawaito shi).

Sai dai shari'ar Musulunci ta shar'antawa mutumin daya fiara aure, yayi sati ɗaya (kwana bakwai) tare da amaryarsa idan budurwa ce, idan kuma bazawara ce, ya kwana uku a wajenta, bayan haka, sai ya raba musu kwana daidai wa daidai, ba tare da wani fifiko ba.

Anas, sahabin Annabi (tsira da amincin Allah su tabbata agare shi) Allah ya yarda da shi yace: “Yin hakan shi ne koyarwar Annabi (tsira da amincin Allah su tabbata agare shi).

Amma fa raba musu kwana baya hana miji wasa ko zantawa da wadda ba ranar kwananta ba, ko shiga dakinta, matufiar dai ba zai sadu da it aba. Domin kuwa Aisha (Allah ya yarda da ita) tace: “Manzon Allah (tsira da amincin Allah su tabbata agare shi) ya kasance yana shiga wajena a ranar kwanan wata, sai yayi abinda yaso dani sai dai ban da jima’i. Duba littafin Irwa’ul Galil na Malam Muhammad Nasiruddin (7/87).

Sannan kuma idan tafiya ta sami mai auren fiye da mace ɗaya yana iya yin fiuri’a a tsakaninsu don warar wadda zai yi tafiyar da ita. Kamar yadda Annabi (tsira da amincin Allah su tabbata agare shi) yake yi a tsakanin matansa.

Imamul Bukhari da Muslim sun rawaici hadisi da aka karɓo daga Aisha (Allah ya yarda da ita) tace: “Manzon Allah (tsira da amincin Allah su tabbata agare shi) ya kasance idan zai yi tafiya yana yin fiuri’a a tsakanin matansa wadda kuri’arta ta fito, sai Annabi (tsira da amincin Allah su tabbata agare shi) ya tafi da ita”.

Waɗannan abubuwa da muka ji, su ne tsarin da Musulunci ya bufiaci magidanta su bi shi a gudanar da zamantakewarsu da matansu.

Idan kuwa abu ya zama ya fita daga cikin ikon mazaje, to ba a ce su ɗorawa kansu yin abin da ba zasu iya yin saba, sannan kuma ba daidai bane, a zarge su da rashin yin adalci, akan abin da aka san cewa basu da iko a kansa.

Bisa ga misali, shari’ar Musulunci bata ɗorawa miji daidaita son da yake yiwa matansa a cikin zuciyarsa ba, saboda sanin cewa yin hakan wani abune da ya fita daga fiarfiashin ikonsa. Don haka Allah Maɗaukaki yace: “Bazaku iya yin adalci (na soyayya) ba a tsakanin mata, ko da kuwa kuna kwaɗayin yin haka. Saboda haka, kada ku karkata dukkan karkata, har ku bar ta kamar wadda aka rataye”.

Sai dai ako yaushe abin da ba a so, bayyanar da karkatar zuciyar a fili, ta yadda har za a iya fahimtar miji yana fifita matarsa wance akan wance, ko kuma wane yana yin biris da hafifiofiin matarsa wance, banda wance. Babu shakka yin hakan ne babba, tun bama ace miji ya mayar da ɗaya daga cikin matansa tamkar mara miji (wato bora) wanda a saboda girman wannan laifi, har sai da aka tanadar wa da mai yinsa azaba ranar lahira.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya yarda da shi) daga Annabi (tsira da amincin Allah su tabbata agare shi) yace: “Wanda yake da mata biyu, sai ya karkata wajen ɗaya, to zai zo ranar alkiyama tsagin jikinsa a shanye” (Ahmad da Abu Dawud da Tirmizi da Nisa’I da Ibn Majah ne suka rawaito shi).

A nan nake cewa, wannan shi ne abin da ya sauwaka na hafifiofiin mace akan mijinta, saura kuma hafifiofiin miji akan matarsa.

Kamar yadda mace take da hafifiofii na dole akan miji, to haka shima miji yake da hafifiofii na dole akan matarsa.

Ga jerinsu kamar haka:

1. Biyayya.
2. Zaman gidan miji.

3. Ayyukan cikin gida.
4. Kula da abubuwa mallakar miji.
5. Hana wanin miji damar shiga gidan miji.
6. Neman izinin miji don yin Azumin nafila.
7. Neman izinin miji a lokacin bufiatar fita.
8. Godiya da yabawa miji.

Hafifiin Biyayya:

Hafifiin biyayya ga miji shi ne mafi girman hafifiofiin da miji yake da su akan matarsa, saboda faɗar Manzon Allah (tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi) cewa: "Da zan umarci wani yayi sujada ga wani (ba Allah ba), to dana umarci mace tayi sujjada ga mijinta (don biyayya gare shi). Tirmizi,Ibn Hibbana da wasunsu ne suka rawaito shi, kuma an karɓo shi daga ayarin sahabbai Allah ya yarda da su.

Don haka, yi- na-yi, bari-na-bari,dole ne akan mace a zamantakewar da mijinta.

**ABUBUWAN DA SUKE HANA MACE BIN MIJI**

A Musulunce, akwai abubuwan da suke hana aiwatar da umarnin miji a duk lokacin da umarninsa ya ci karo dasu. Ga bayanin abubuwan kamar haka:

1. Umarni da saɓon Allah: Haramun ne mace tayi wa mijinta biyayya a duk lokacin da ya umarce ta da aikin saɓo, saboda hadisin da aka karɓo daga sahabin Annabi, Aliyu (R.A) yace, Manzon Allah (tsira da amincin Allah su tabbata agare shi) yace: "Babu biyayya ga wani mutum a cikin aikin saɓo. Hafiifia kaɗai ana yin biyayya ne a cikin abin da yake sananne a shari'a ".

Bukhari, Muslim da Abu Dawud da wasun su ne suka rawaito shi.

2. Umarni da abin da yafi fiarfin ikon wanda aka umarta. Musulunci bai yarda mace ta aiwatar abin da mijinta yasa ta matufiar dai abin da yasa ta yin yafi fiarfin ikonta. Dalili kuwa hadisin da aka karɓo daga Umar ɗan Khaddab (R.A) cewa: " (mu musulmai an hana mu ɗorawa kanmu abinda bazamu iya ba". Bukhari ne ya rawaito shi.
3. Afkuwar fiafifiarfan uzuri: kamar mantuwa ko rashin lafiya. A musuluce, mantuwa da rashin lafiya fiafifiarfan uzuri ne daka iya hana mace aiwatar da umarnin mijinta, kuma ya zama batayi laifi ba, amma fa duk lokacin da mace tafii bin umarnin mijinta, alhali umarnin nasa bai ci karo da ɗaya daga cikin waɗannan abubuwa ba, to babu ko shakka ta tabbata mai saɓo kuma ta cuci kanta .

**HAKKIN ZAMAN GIDAN MIJI**

Tabbatar mace cikin gidan mijinta doka ce tabbatacciya daga Allah Maɗaukaki, ga abin da Allah yace: "(ku mata) ku tabbata cikin gidajenku, kada ku bayyanar da adonku irin bayyanar da adon maguzancin farko".

Bisa dogaro da wannan ayar, haramun ne mace ta fita daga gidan mijinta ba tare da izininsa ba, ko da kuwa ta lefia waje ne.

Wannan yasa wani ɗan uwa ya gargaɗi mata da cewa:

Sai ta ukunsu gadangama ke nan,

Ba ta nufin gyara sai cuta.

Bata nufin khairi ga mijinta,

Baga kishiyoyi ba ga mafiotaba.

Ba ta nufin gyara sai ɓarna,

Sai duka safe ta cuci mijinta.

Ya tafi ofis ko kuma kanti,

Ba ta fiara zama ɗakinta.

In mai noma ne ko zage,

Ka tafi gona zaure za ta.

Ta na neman taga masu wucewa,

Wai ita dai suga kyan fuskarta.

In taga sunfii shiga harkar ta,

Sai kaji tace zata mafiobta.

**AYYUKAN CIKIN GIDA**

Imamul Bukhari da Muslim sun rawaici hadisi da aka karɓo daga Abdullahi ɗan Abbas, Allah ya yarda da su, daga Annabi (tsira da amincin Allah su tabbata agare shi) yace: “Dukkanku makiyaya ne, kuma dukkanku ababan tambayane game da abubuwan kiwonku,…. Mace ma makiyayiya ce akan gidan mijinta da ‘ya’yansa, kuma ita ma abar tambayace game da abubuwan kiwonta”.

Sannan an karɓo hadisi daga Asma’u ‘yar Abubakar Siddik, Allah ya yarda dasu tace: “Na kasance ina yi yiwa zubairu (mijina) hidindimun gida baki ɗaya, kuma ya kasance yana da wani doki da nake wahala da shi, ina yi masa ciyawa kuma ina kula da shi”. Iman Ahmad ne ya rawaito shi.

A wata ruwayar kuma (Asma’u) ta fiara da cewa, tana ɗinke guga, da kwaɓa gari. Ahmad ne ya rawaito shi.

Sannan kuma dai an karɓo hadisi daga Aliyu, Allah ya yarda da shi, yace, hafiifia matarsa Faɗima data sami labarin an kawowa Annabi (Tsira da amincin Allah ya su tabbata agare shi) bayi, sai taje gida domin ta kokawa Annabi (tsiri da amincin Allah su tabbata agare shi) game da kantar da hannunnta yake yi a sakamakon amfani da dutsen nifia (ko ya agaje ta da baiwa), da bata sami Annabi (tsira da amincin Allah su tabbata agare shi) a gida ba, sai ta gayawa Aisha (R.A), da Annabi (tsira da amincin Allah su tabbata agare shi) ya dawo, sai Aisha ta faɗa masa safion Faɗima, sai Annabi (tsira da amincin Allah su tabbata agare shi) ya tafi gidan ‘yarsa Faɗima; ko da ya isa sai ya tarar da ita da mijinta Aliyu (R.A) Sun riga sun kwanta bacci, da suka yunfiura zasu ta shi domin taro shi, sai yace dasu kuyi zamanku a inda kuke, sannan sai ya zauna kuma yace dasu: “Ashe bana sanar daku abin da yafi wanda kuka tambaya ba, idan zaku kwanta bacci kuyi tasbihi talatin da uku, hamdala talatin da uku, takbir kuma sau talatin da huɗu”. Bukhari da Muslim ne suka rawaito.

Duba da waɗannan dalilai da wasunsune wasu daga cikin malamai suka yanke hukuncin cewa: ɗaukar ɗawainiyar aikace-aikacen da suka shafi cikin gida nauyi ne daya rataya a wuyan matar aure.

Ko da yake ba laifi bane a shari'ance ga wanda yake da iko ya samo wa matarsa 'yar aiki, sai dai faba ita ba samun ladan da ake bawa waɗanda suka tsayu da kansu domin aiwatar da waɗannan ayyuka na cikin gida

yaku 'yan uwa mata! ku sani fa ba fiasfianci bane ku tsayu da:

- Ba wa dabbobin miji abinci da kuma share garkensu.
- Wanke banɗaki.
- Sharar tsakar gida.
- Dafa abinci.
- Gyara shimfiɗa.

Da sauran su.

Waɗannan abubuwa dukkansu share fagen shiga Aljanna ne, shi yasa Annabi (tsira da amincin Allah su tabbata agare shi) da sahabbansa basu goyi bayan 'ya'yansu da matansu suyi watsi ko sakaci dasu ba. Wannan ke nan.

**KULA DA ABUBUWA MALLAKAR MIJI**

I, tabbas ne dukkan wasu abubuwa mallakar miji da suka haɗar da kuɗinsa, abincinsa, kadarorinsa, kayan aiwatar da sana'arsa da dai sauran su; kowanne yana ɗaya daga cikin abubuwan da Allah zai tambayi mace game dasu a lahira. Don haka da mai kulawa, da mai banzatarwa, da mai sacewa, duk zasu amsa tambayar Allah ba fasawa.

**HANA WANIN MIJI SHIGA GIDAN MIJI**

Ya inganta cikin bayanan Manzon Allah (tsira da amincin Allah su tabbata agare shi) a hajjinsa ta bankwana yace: "Hafiifia maza kuna da hafifii akan mata, na kada su kuskura suyi izinin shiga gidajenku ga wanda ba kwaso ya shigar muku gida, kuma kada su bar wani ya hau muku shinfiɗa alhali ba kwaso". Muslim ne ya rawaito shi, kuma an karɓo shi ne daga sahabin Annabi (tsira da amincin Allah su tabbata agare shi) wato jabir, Allah ya yarda da shi.

Kuma an karɓo daga Abu Huraira, Allah ya yarda da shi yace: "Hafiifia Manzon Allah (tsira da amincin Allah su tabbata agare shi) yace: "Baya halatta wata mace tayi izinin shiga gidan mijinta, sai da izininsa". Bukhari ne ya rawaito shi.

**NEMAN IZININ MIJI DON YIN AZUMIN NAFILA**

Bukhari,Muslim, Abu Dawud, Nasa'I da wasunsu sun rawaito hadisi da aka karɓo daga Abu Huraira (R.A) Yace: Manzon Allah (tsira da amincin Allah su tabbata agare shi) yace: "Bai halatta ba mace tayi Azumi mijinta na nan agari in ba Azumin Ramadan ba".

Sannan kuma ko Azumin Ramadan ɗin, in dai na ramuwa ne, bai halatta mace tayi shi ba har sai ta sanar da mijinta, ta nemi izininsa saboda yalwar kwanakin da take dasu game da ramuwar Azumin da ake bin ta ɗin.

**NEMAN IZININ MIJI A LOKACIN BUKATAR FITA**

A zamanin Manzon Allah (tsira da amincin Allah su tabbata agare shi) da zazzaɓi ya tsananta ga matarsa Aisha (R.A) a dalilin fiagen zina da aka yi mata, ta nemi Manzon Allah (tsira

da amincin Allah su tabbata agare shi) da yayi mata izinin tafiya gidansu, domin ta sami tabbacin shin abin da ake faɗa game da itan ya isa kunnen iyayenta kuwa? Don kuma ta dace da samun lallashin mahaifanta da tausayawarsu. Sai Manzon Allah (tsira da amincin Allah su tabbata agare shi) yayi mata izini ta tafi gida…" sahihul Bukhari, hadisi na (4750).

**GODIYA DA YABAWA MIJI**

Yana daga cikin kyawawan halayen Musulmi fiwarai ya zama mai yin tukuici da godiya da yabawa kana bin kirkin da aka yima.

Manzon Allah (tsira da amincin Allah su tabbata agare shi) yace: "Duk wanda yayi muku abin kirki, to kuyi masa tukuici, idan ba ku sami abin yi masa tukuici ba, to kuyi masa addu'a, har sai kun ga cewa kun saka masa (wato da yin addu'ar)".

A wata ruwayar kuma Manzon Allah (tsira da amincin Allah su tabbata agare shi) cewa yayi: "Duk wanda aka yi masa abin kirki sai yace da wanda yayi masa kirkin Allah ya saka maka da alheri, to hafiifia ya kai matufia wajen yabawa". Tirmizi, Nisa'I da Ɗabarani ne suka rawaito shi.

To 'yar albarka yi da gaske kiyi aiki da wannan koyarwa ta Manzon Allah (tsira da amincin Allah su tabbata agare shi) ki yabawa mijinki game da ɗumbin alherin da yake yi miki, sai ki rabauta da kyakkyawan sakamakon Allah (S.W.T), kuma ki fiara kima da daraja a wajen mijinki, sannan kuma ki kubuta daga faɗawa cikin jerin mata butulu waɗanda Manzon Allah (tsira da amincin Allah su tabbata agare shi) yace da ire-irensu Allah baya duban matar da ba ta godewa mijinta, alhali ba zata iya wadatuwa daga shi ba". Nasa'I ne ya rawaito.

Kuma an karɓo shi ne daga Abdullahi ɗan Amr(R.A) wani fiarin abin ban tsoro ita wannan ta'ada ta butulci ita ce sanadiyyar yawaitar mata a cikin wuta kamar yadda ya tabata a hadisin da aka karɓo daga Abdullahi ɗan Abbas (R.A), daga Annabi (tsira da amincin Allah su tabbata agare shi) yace: "Na hangi cikin wuta, ban taɓa ganin abin ban tsoro ba irin na yau, kuma naga mafi yawaicin 'yan cikinta mata ne. sahabbai sukace: "Meyasa ya Manzon Allah ? yace: "saboda suna butulcewa". Aka ce Allah suke butulcewa ?yace: Miji suke butulcewa, kuma suna da butulcewa kyautatawa, da zaka ga kyautatawa ɗayarsu tsawon shekara, sannan taga wani abin da bai mata daɗi ba daga gare ka, sai kaji ta ce: "tun da take baka taɓa ganin wani alheri ba daga gare kaba". Bukhari ya rawaice shi. Hadisi mai lamba (5197).

To 'yar uwa ki kiyayi cewa da mijinki me ya taɓa tsinana miki? kin dai ji irin abin da faɗar hakan ke jawowa.

**HAKKOKIN DA MA'AURATA SUKE TARAYYA A KANSU**

A musulunce ma'aurata nayin tarayya akan hafifiofii masu zuwa kamar haka:

1. Taimakawa junansu akan bin Allah (S.W.T).
2. Kyautata zamantakewa.
3. Hafiuri da juna.
4. Biyawa junansu bufiatar sha'awa.
5. Rufa wa junansu asiri.
6. Kishin junansu.
7. Kula da tsafta da kwalliya.

8. Mutunta dangin kowannensu.
9. Kyautata tarbiyyar ‘ya’yansu.

Ga bayanin waɗannan hafifiofii nan tafe ɗaya bayan ɗaya a fayyace:

1. Taimakawa junansu akan Bin Allah:

An karbo hadisi daga Abu Huraira (R.A) yace, Manzon Allah (tsira da amincin Allah su tabbata agare shi) yace: “Allah ya jifian mutumin da zai tashi cikin dare sai yayi salla, kuma ya tashi matarsa domin tayi sallah, in tafii tashi ya yayyafa mata ruwa a fuskarta, kuma Allah ya jifian matar daza ta tashi cikin dare sai tayi salla, kuma ta tashi mijinta domin yayi salla, in yafii tashi ta yayyafa masa ruwa a fuskarsa”. Abu Dawud, Nasa’I, Ibn Majah da wasunsu ne suka rawaito shi.

Kuma an karɓo daga Abu Sa’id (R.A) y ace: Manzon Allah (tsira da amincin Allah su tabbata agare shi) yace: “Idan mutum ya tashi iyalansa cikin dare suka yi salla za a rubuta su cikin maza da mata, masu ambaton Allah da yawa”. Ibn Majah ya rawaito shi.

Sannan kuma an karɓo daga Aisha (R.A) tace: “Mun kasance muna tanada wa Manzon Allah (tsira da amincin Allah su tabbata agare shi) aswaki da ruwan alwalarsa, sai Allah ya tashe shi a sanda yaso tashinsa cikin dare, sai ya goge bakinsa kuma yayi alwala, sannan yayi salla”. Ibn Hibban ya rawaito.

2. Kyautata Zamantakewa:

Wannan hafifii na kyautata zamantakewar ma’aurata ya fiunshi abubuwa da dama da suka haɗar da:

(a) Cin abinci tare.
(b) Zantawa da juna.
(c) Yin wanka tare.
(d) Wasa da dariya.
(e) Gudanar kyautar a tsakaninsu.

Da dai sauran abubuwan da suke kyautata zaman tare.

(a) Cin Abinci Tare:

An karbo daga Aisha (R.A) tace: “Manzon Allah (tsira da amincin Allah su tabbata agare shi) ya kasance yana zuwa da abin sha sai in sha daga mazibin abin shan alhali ina yin haila, sannan sai manzon ya karba ya sanya bakinsa a gurin danasa bakina ya sha, kuma na kasance ina ɗaukar kashi mai nama in gwagwiyi, sannan ya karba sai ya sanya bakinsa a inda nasa bakina shi ma ya gwagwiya”.

Sannan Imamul Bukhari da Muslim sun rawaici hadisi da aka karɓo daga sa’ad ɗan Abi Wafifias (R.A) daga Annabi (tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi) yace da shi: “Hafiifia babu wata ciyarwa da zaka nufi Allah da ita face sai an baka lada a kanta, har lomar da kake sanyawa a cikin bakin matarka”.

Ina angwaye da tsofaffin hannu a harkar aure cikinku wane ne yake bawa matarsa abinci a baki? Kuma wane ne yake sanya bakinsa a inda matarsa tasa nata bakin; ya ci abin da ta ci ko kuma ya sha

abin da ta sha? Tare da cewa yin hakan shi ne koyarwa da Manzon Allah (tsira da amincin Allah su tabbata agare shi) yayi mana.

Ina mazan da idan matansu suna haila ko kuma biki basa iya zama akusa dasu; ballantana suci wani abu tare da su, shin su irin waɗannan mazan dawa suke yin koyi ne? Manzonmu dai bai yi haka ba, kuma mu al'ummarsa bai umarce mu da yin haka.

(b) Zantawa da juna:

Manzon Allah (tsira da amincin Allah su tabbata agare shi) yace: "Daddadar kalma sadaka ce". Bukari da Muslim ne suka rawaito a hadisin da aka karɓo daga Abu Huraira (R.A).

Don haka zantawar ma'aurata da kalmomin da zasu faranta wa junansu rai dasu, yana daga cikin fiofofin alherin duniya da lahira da rayuwar aure ta fiunsa.

A duniyance, yin hakan zai fiarawa ma'aurata nishaɗi da fiaunar juna, a lahirance kuma zai tara musu ladan sadaka da zasu girba.

Wani abin ban sha'awa Manzon Allah (tsira da amincin Allah su tabbata agare shi) ko wajen faɗar sunan matarsa sai yayi salon da zai faranta mata rai, kamar yadda aka karɓo hadisi daga Abu salama ɗan Abdurrahman yace: "Hafiifia Aisha matar Annabi (tsira da amincin Allah su tabbata agare shi) tace: Manzon Allah (tsira da amincin Allah su tabbata agare shi) yace da ita "Ke Aish jibril yana yi miki sallama". Bukhari ne ya rawaito (hadisi mai lamba (6201) da mai lamba (827) cikin littafinsa Al'adabul Mufrad.

(c) Yin wanka Tare:

Daga Aisha (R.A) tace: "Na kasance ina yin wankan janaba nida Manzon Allah (tsira da amincin Allah su tabbata agare shi) daga mazubi guda dake Tsakani na da shi, hannayenmu na sassaɓawa a cikin mazubin, sai ya riga ni har sai nace da shi bar min saura, bar min sauran". Bukhari da Muslim da Abu Awana ne suka rawaito shi.

Tambaya: wai kuwa tun da kuka yi aure, kun taɓa yin wanka tare? In kai ne baka bata fiofar yin haka ba; to ka gyara, idan kuma kece baki waye da anayin haka ba, to kiyi fiofiari ki waye da yin aiki da wannan sunna don kyautata auratayyarku.

(d) Wasa da Dariya:

Wata rana Manzon Allah (tsira da amincin Allah su tabbata agare shi) ya tambayi sahabinsa jabir ɗan Abdullah yace da shi: "jabir kayi aure? Yace: "I". (nayi aure). Sai yace: "Budurwa ko bazawara?" nace: "A'a bazawara ce". Ya ce: "Ina ma buburwace ka rinfia wasa da ita, itama ta rinfia wasa da kai, ka rinfia sata dariya, ita ma ta rinfia saka dariya…". Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi.

An karɓo daga Aisha (R.A) tace: Ta kasance tare da Annabi (tsira da amincin Allah su tabbata agare shi) a wata tafiya a lokacin ina amarya ban yi jiki ba, sai yace da sahabbansa su yi gaba; sai suka yi gaba, sannan sai yace da ni: "Zo muyi yi tsere". Sai muka yi tsere na wuce shi, bayan haka sai na kuma fita wata tafiya tare da shi, sai yace da sahabbansa suyi gaba, sannan yace dani: "Zo muyi tsere". Na manta da munyi tsere na wuce shi, kuma yanzu nayi jiki, sai nace ta yaya zan yi tsere da kai a wannan yanayin da nake ciki? Sai yace ai kuwa sai kinyi. Sai muka yi ya wuce ni, kuma ya rinfia

dariya, sannan sai yace: "Ɗaya da ɗaya". Humaidi da Abu Dawud da Nasa'I da wasunsu ne suka rawaito shi.

'yan uwa ma'aurata ba fa sai lallai wasan tsere ba, akwai wassanni salo-salo iri daban daban da zaku iya yi don nishaɗantarwa da kyautata zamantakewar juna.

**(e) Gudanar Kyauta Tsakanin Ma'aurata**

Imamul Bukhari ya rawaici hadisi a cikin littafinsa- Al'adabul Mufrad, wanda aka karɓo daga Abu Huraira, Allah ya yarda da shi, daga Annabi (tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi) yace: "ku rinfia yin kyauta sai ku rinfia son junanku".

Wannan hadisi na koyar da mu ribatar halayyar kyauta don fiarfafa soyayyarsu da fiara fiaunar junanmu, ke nan idan ma'aurata suka dabi'antu da halayyar yiwa junansu kyauta; to kauna da soyayyarsu za su fiarfafa kamar yadda zamantakewarsu zata fiara kyautata.

Amma fa kada hakan yasa ma'aurata su manta da cewa tushen soyayyarsu fa neman yardar Allah ne da raya sunnar Manzon Allah (tsira da amincin Allah su tabbata agare shi), ba a abin da ɗayansu zai ba wa ɗayan ba. 'Yan uwa muddin muka tsayu akan haka tsaikon samun abin hannun dayanmu ba zai gurɓata zamantakewar aurenmu ba. Wannan ke nan.

3. Hafiuri da Juna:

Allah (S.W.T) yace: "Yaku waɗanda kuka bada gaskiya ku nemi taimako da hafiuri da salla (cikin al'amuranku), hakika Allah na tare da masu hafiuri".

Kuma dai Allah (S.W.T) yace: "kayi hafiuri akan duk abin daya same ka, hafiifia hakan na daga cikin muhimman al'amura".

Sannan kuma an karbo hadisi daga Abdullahi ɗan Umar, Allah ya yarda dasu, yace: "Manzon Allah (tsira da amincin Allah su tabbata agare shi) yace: "Muminin da yake cuɗanya da mutane kuma yake hafiuri da cutarsu, shi ne yafi alheri akan muminin da baya cuɗanya da mutane kuma baya hafiuri da cutarwarsu". Ibn Majah ne ya rawaito shi.

Duba da waɗannan dalilai hafiuri ya zamar mana dole matufiar dai muna son samun taimakon Allah da zamantowarmu mafiya alherin bayi.

Don haka mita da fushi da raki duk ba za su maganta mana ɓacin ran da abokin zama ya sabbaba mana ba. Mafita kawai shi ne hafiuri da bin al'amura sannu a hankali. "Hafiuri maganin zaman duniya". "Mahafiurci Mawadaci".

**4. Biyawa Junansu Buƙatar Sha'awa:**

Abu ne sananne ga kowa cewa, Allah (S.W.T) ya halicci jinsin maza da ɗabi'ar sha'awar jinsin mata, kamar yadda ya halicci mata da sha'awar jinsin maza. Sannan da yake Allah Gwani ne mai hikima cikin al'amuransa, sai ya shar'anta wa bayinsa aure domin ya zama halattacciyar hanyar da ya yarje musu bin ta don cimma biyan bufiatarsu ta sha'awa. Wanda a sakamakon haka maza suka zama kariya da sutura ga mata kamar yadda su ma matan suka zamar wa maza kariya da sutura. Allah (S.W.T) yace: "… su mata sutura ce gare ku, haka kuma maza sutura ce gare su…".

Kuma an karɓo hadisi daga Abdullahi ɗan Mas'ud, Allah ya yarda da shi yace, Manzon Allah (tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi) yace: "Hafiifia aure yafi sa rintse ido (daga kallon haram), kuma yafi zama kariya ga tsiraici (daga afkawa haram) wato zina". Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi.

Saboda haka sai kowane ɗaya daga cikin ma'aurata ya tsayu da gaske wajen sauke wannan hafifii na biyan bufiatar sha'awa zai amsa sifarsa ta zamowa abokin zamansa kariya da sutura. Ga mai son ya bayar da wannan hafifii kuwa daidai da yadda Musulunci ya tsara, to ga abin daya kamata yayi kamar haka:

1. Tsaftace baki kafin kusantar abokin biyan bufiatar sha'awa.
2. Gabatar da wasa da taɓa gurare da ke motsa sha'awa, kamar sumba, runguma, da sauransu.
3. Yin addu'a da ambaton Allah kafin fara biyan bufiatar sha'awa.
4. Wadatuwa da kafar da Allah ya amince a sadu da ita.
5. Nisantar saduwa a lokacin zubar jinin al'ada, da na haihuwa.
6. Nisantar saduwa ta dubura.

Wanda ya kiyaye waɗannan dokoki da tsare-tsare ya halatta ya zai ɓi salon daya so don aiwatar da biyan bufiatar sha'awarsa a tsaye ne ko a tsugune ko kuwa a kwance.

Don fiara samun nutsuwa game da dalilin waɗannan dokoki kuwa ga bayanansu kamar haka:

An karbo daga Shuraih ɗan Hani'I yace, nace da Aisha: Wane abu Annabi (tsira da amincin Allah su tabbata agare shi) yake fara yi idan ya shigo gidansa? Sai tace: "Aswaki yake fara yi". Muslim ne ya rawaito shi.

Bayan haka a bayanan da suka gabata, munji cewa, Annabi (tsira da amincin Allah su tabbata agare shi) yace da sahabinsa jabir a lokacin daya auri bazawara. "inama budurwa ka aura wacce zaka ringa wasa da ita, ita ma tana wasa da kai, kuma kana sata dariya itama tana saka dariya".

Kuma an karbo daga abdullahi ɗan Abbas Allah ya yarda da shi yace, Manzon Allah (tsira da amincin Allah su tabbata agare shi) yace: "Da ɗayanku lokacin da zai sadu da iyalinsa zai ce: ya Allah ka nesantani daga shaiɗan ka kuma nesanta shaiɗan daga abin daka azurta ni da shi". To da idan aka azurta su da samun da ta dalilin wannan saduwa shaiɗan ba zai cutar da shi ba har abada". Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Abbas Allah ya yarda da shi yace, Manzon Allah (tsira da amincin Allah su tabbata agare shi) yace: "Allah baya duban rahama ga mutumin daya sadu da wani na miji ko mace ta dubura". Tirmizi ne ya rawaito shi.

Sannan Allah (S.W.T) yace:

"kuma suna tambayar ka game da jinin haila kace (da su) shi fiazanta ne (don haka) ku nisanci saduwa da mata a lokacin haila kada ku kusance su har sai sunyi tsarki…". Bafiara, aya ta 222.

Kuma dai Allah (S.W.T) yace: "Matanku mashukar 'ya'yanku ne, to ku zowa mashukarku ta yadda kuka so". (wato matufiar dai ta kafar da aka halarta muku saduwa da sune".

**HAƊARIN KIN SAURARAR MIJI IN YA SO**

## BIYAN BUKATAR SHA’AWA

An karɓo daga Abu Huraira, Allah ya yarda da shi yace, Manzon Allah (tsira da amincin Allah su tabbata agare shi) yace: “Idan mace ta kwana tana mai fiauracewa shimfiɗar mijinta, Mala’iku zasu yi ta tsine mata har ta wayi gari”. Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi.

## RUFAWA JUNANSU ASIRI

Sirri shi ne ɓoye abin da babu wata masalaha ko amfani cikin bayyanar da shi, kuma ɗabi’antuwar ma’aurata da ita wannan kyakkyawar halayya ta rufin asiri wani babban jigo ne game da tabbatuwar inganci da karantar matsaloli tattare da rayuwarsu ta aure dama watarta.

Don haka lallai ne ma’aurata su sani ba duk abin daya shafi rayuwar aurensu ya halatta su bayyana ga waninsu ba, abin ya shafi maganganunsu ne ko kuwa ya shafi ayyukan da suka gudanar ne.

Bisa ga misali, an karɓo daga Asma’u ‘yar Yazid Allah ya yarda da ita tace: Na kasance a wajen Manzon Allah (tsira da amincin Allah su tabbata agare shi) a lokacin maza da mata na zaune a wajensa sai ya ce: “Mai yiwuwa wani na faɗar abin da yake aikatawa da iyalinsa kuma mai yiwuwa wata na bada labarin abin da take aikatawa tare da mijinta sai kowa yayi shiru, sai ni kuwa nace: “I wallahi ya manzon Allah matan na faɗa, kuma mazan ma suna faɗa. Sai yace: to kada ku fiara faɗa, hafiifia faar hakan kamar wani watsattse ne ya haɗu da wata watsattsiya a tsakiyar hanya ya afka mata mutane na kallon”. Imam Ahmad ne ya rawaito shi.

Kuma an karɓo daga Abi Sa’idil khudri Allah ya yarda da shi yace, Manzon Allah (tsira da amincin Allah su tabbata agare shi) yace: “Daga cikin mafiya sharrin matsayi a Wajen Allah ranar Alkiyama akwai mutumin da zai keɓe ya kaɗaita da matarsa ita ma ta kaɗaice da shi, sannan yaje ya yaɗa sirrinta”. Muslim da Ahmad ne suka rawaito shi.

Saboda haka, rashin kulawa da wannan hafifii zubar da mutunci ne a duniyance, kuma jefa kai ne cikin mummunar rayuwa a lahira, Allah ka tsare mu. Amin

## KISHIN JUNANSU

Kishi wata kyakkyawar sifa ce daga cikin kyawawan siffofin bayin Allah na fiwarai.

Kishin ma’aurata kuwa a junansu shi ne: bayyanar da damuwar ɗayansu da ɓacin ransu akan ɗaya a duk lokacin daya durfafi abin da zai gurɓata musu addini ko zai zubar musu da mutunci.

Don haka ba daidai bane miji ya zurawa matarsa ido ya barta tana wasa da addini, ko aikata sakarci da shirme. Haka kuma bai dace ba mace tayi biris ta kauda kai daga ayyukan assha da mijinta yake aikatawa ba.

Idan kuwa ma’aurata sukayi sakacin kula da wannan hafifii, to sun tabbata marasa kishin junansu, wanda a fiarshe hakan na iya kai su gayin rayuwa irin ta dabbobi inda zaka ga mace na sanya gabanta inda take so, shima kuma mijin na yin duk abinda yaga dama. Wannan Kenan.

Sannan kuma zaman ma’aurata cikin zargin junansu da tare dafaruwar wani fiwafifiwaran abin zargi ba, ya saɓa da koyarwar addininmu na musulunci da tsarin zamantakewa. Saboda haka bai halatta a rinfia samun haka a tsakaninmu ba.

An karɓo hadisi daga Jabir ɗan Atik Allah ya yarda da shi yace: “Hafiifia Annabi (tsira da amicin Allah su tabbata agare shi) yace: “…kishin da Allah baya so shi ne kishi ba tare da wani abin zargi ba”. Abu Dawud ne ya rawaito shi.

**KULA DA TSAFTA DA KWALLIYA**

Babban abin birgewa game da wannan hafifii datar da wanda ya tsayu akan tabbatuwarsa da damun fiaunar Allah (S.W.T).

Wani fiarin abin ban sha’awa kuma Allah ya halicci bayinsa da ɗabi’ar son abu mai kyau da tsafta, ke nan bayan fiaunar Allah da mai tsafta yake samu, zai rabauta kuma da samun dandazon masoya daga cikin bayin Allah.

Allah (S.W.T) yace: “…hafiifia Allah yana son (bayinsa) masu yawan tuba, kuma yana son (bayinsa) masu tsarki”.

Kuma an karɓo daga Abdullahi ɗan Mas’ud Allah ya yarda da shi, daga Annabi (tsira da amincin Allah su tabbata agare shi) yace: “…hafiifia Allah kyakkyawa ne, kuma yana son kyu…”. Muslim ya rawaito shi.

Don haka wayayyun ma’aurata basa wasa da wannan hafifii na tsafta da kwalliya.

Batun abubuwan mallaka.

**TSAFTAR JIKI DA KWALLIYARSA:**

Tsaftar jiki ta fiunshi yin wanka a kai a kai, goge baki, aske gashin hammata dana mara, yanke farata, da rage gashin baki ga namiji.

Kwalliyar jiki kuwa kamar sa kwalli, dasa zobe, shafa mai, taje kai ko kitse shi ga mace, da yin fiunshi, sanya sarfia, ko ɗan kunne ko kuma awarwaro, da sauran abubuwan da ba suci karo da fia’idojin addininmu ba.

Bai halatta Musulmi ya canja halittar da Allah yayi masa ba da sunan kwalliya, kamar yin tsage (shasshawa, da fashin goshi, da bille, da makamantansu), fiona gashi da fiara shi, da fifie hafiori da yin bilicin da cisge furfura ko rina ta ta koma bafia, duk waɗannan yin su haramun ne ga musulmi.

**TSAFTAR SUTURA DA KWALLIYARTA**

Tsaftar sutura shi ne wanke ta, kwalliyarta kuma ya fiunshi yi mata ado, da goge ta, da sanya turare, da karya hula. Da dai makamantansu, matufiar dai basu saɓa fia’idojin addininmu ba.

**TSAFTAR GIDA DA ABUBUWAN MALLAKA**

Tsaftar gida da abubuwan mallaka kuwa su ne wanke abin wankewa, da share na sharewa da goge na gogewa da tsara na tsarawa. Mai gida ya yi nasa, (kamar yashe kwata), uwar gida da amarya masu yi nasu. Wannan ke nan.

**MUTUNTA DANGINSU**

Kyautata hulɗar miji da dangin matarsa (wato surukansa); da kuma kyautata huldar mace da dangin mijinta, abu ne mai tushe da asali a Musulunci.

An karɓo daga Aliyu ɗan Abu Ɗalib Allah ya yarda da shi yace: "Na kasance mutum mai yawan fitar da maziyyi, sai na ji kunyar tambayar Manzon Allah (tsira da amincin Allah su tabbata agare shi) (hukuncinsa), saboda matsayin 'yarsa (na kasancewar ta mata) a gare ni, sai na umarci Mifidad ɗan Aswad ya tambayar mini shi, sai ya tambaye shi, sai Manzo yace: "Zai wanke tsiraicinsa ne kuma ya yi alwala". Bukhari da muslim ne suka rawaito shi.

Wannan ya sa malamai suka ce: Jin kunyar siriki da yi masa ladabi tsare hafifii ne daga cikin hafifiofiin da Musulunci ya bufiaci a ba wa surukai.

Sannan kuma Imam Muslim ya rawaici hadisi da aka karɓo daga Aisha Allah ya yarda da ita ta ce: Halatu 'yar Khuwailid 'yar' uwar Khadija ta nemi izinin shiga wajen Manzon Allah (tsira da amincin Allah su tabbata agare shi) sai ya tuna neman izinin (matarsa) Khadija, sai ransa ya yi fari ya nuna farin cikinsa da zuwan Halatu, sannan yace: "Ya Allah ga Halatu 'yar Khuwailid ka taimake ta ka zama gatanta…".

Shi kuma wannan hadisi na sanar da mu cewa ko bayan mutuwar matar da mutum ya aura danginta na da hakkin a ci gaba da mutunta su da darajanta su, to ina ga kuma a ce tana raye kuma ana tare da ita.

**Kyautata Tarbiyyar 'Ya'ya**

'ya'ya wata babbar ni'ima ce da baiwa da Allah yake yin ta ga wanda yaso cikin bayinsa.

Yaba wa Allah da gode masa game da wannan ni'ima shi ne: uwa da uba; miji da mata, su tsayu a kan tarbiyantar da 'ya' yansu da ilmantar da su hakkokin Allah da na bayinsa don su iya isarwa da kowane mai hakki hakkinsa.

Allah (S.W.T) ya labarta mana yadda Annabi Ibrahim da Annabi Ya'akub (A.S) suka yi kokarin sauke wannan nauyi da ya rataya a wuyansu inda ya ce:

**Ma'ana:*"kuma ba wanda zai ƙi addinin Annabi Ibrahim sai wanda bai san ciwon kansa ba. Hakika mun zaɓe shi a duniya kuma shi a lahira yana cikin salihai (130). (ku tuna) lokacin da Ubangijinsa yace da shi ka mika wuya (ka musulunta) ya ce "na mika wuya ga Ubangijin talikai (131). Sai kuma (Annabi) Ibrahim ya yi wa 'ya'yansa wasiyya da ita (wannan hanyar), kuma Ya'akub ma (ya yi wasiyya), ya ce: "ku 'ya'yana! Hakika Ubangiji ya zaɓa muku addini, saboda haka kada ku kuskura ku mutu sai kuna musulmai (132)".***

Ita ma kakar Annabi Isa (A.S) matar Imran ta tsayu da yi wa 'yarta Maryam addu'ar Allah ya tsare ta kuma ya tsare zuriyarta daga sharrin shaidan. Allah Madaukaki ya ce:

**Ma'ana: *"…hakiƙa na raɗa mata suna Maryam, kuma (ya Ubangijina) ina rokonka ka tsare ta da zuriyarta daga shaidan jefaffe (36). Sai Ubangiji ya karbe ta kyakkyawar karba, kuma ya haɓaka, kuma ya sanya rainonta ga Zakariyya…".***

Don haka, rainon 'ya'ya a kan tarbiyyar fiwarai da ta fiunshi dukkan wani abu kyakkyawa a musulunce, tare da nesanta su daga dukkan wani mummunan abu a musulunce; hafifii ne ya rataya a kan miji da mata, uwa da uba gaba ɗayansu, lallai ne su yi da jikinsu, da maganarsu, da kuma dukiyarsu har a kai ga cim ma biyan bufiata.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Umar Allah ya yarda da su, daga Annabi (tsira da amincin Allah su tabba agare shi) ya ce: "Dukkanku makiyaya ne kuma kowannenku abin tambaya ne a kan abin da aka

ba shi kiwo… mai gida makiyayi ne a kan mutanen gidansa, mace ma makiyayiya ce akan gidan mijinta da ‘ya’yansa, dukkanku makiyaya ne kuma dukkanku ababan tambaya ne a kan abin da aka ba ku kiwo”. Bukhari da muslim ne suke rawaito shi.

**HAKKIN WANDA MUTUWA TA RABA SHI DA**

**ABOKIN ZAMANSA DAGA CIKIN MA’AURATA**

A musulunce idan mutuwa ta raba tsakanin ma’aurata, to wanda yake raye cikinsu yana da haKKi daga cikin abin da wanda ya mutu ya bari; Idan mace ce ta mutu ta bar mijinta, to mijin zai gaji rabin abin da matarsa ta mutu ta bari na abubuwan mallakarta, idan ba ta da ɗa a raye. Idan kuma tana da ɗa a raye, to mijin nata zai gaji ɗaya bisa huɗun abin da ta mutu ta bari ne. Allah (S.W.T) ya ce:

“kuma kuna da rabin abin matanku suka bari idan ba su da ɗa,amma idan suna da ɗa, to kuna da ɗaya bisa huɗu daga abin da suka bari, bayan (an zartar da) wasiyya da suka yi, ko kuma bashin da ke kansu…”.

Idan kuwa miji mutuwa ta ɗauke shi ta bar mata, to ita matar za ta yi wa mijin takaba, sannan kuma zata gaji ɗaya bisa huɗun abin da yabari idan ba shi da ɗa a raye, idan kuma yana da ɗa a raye, to zata gaji ɗaya bisa takwas daga abin da mijinta ya mutu ya bari, wannan shi ne abin da mace ke gada daga miji ko da kuwa su nawa ya mutu ya bari a matsayin matansa.

Allah (S.W.T) ya ce: “…su kuma (matan aure) suna da rabo ɗaya bisa huɗu na abin da kuka bari idan ba su da ɗa. Amma idan kuna da ɗa, to suna da ɗaya bisa takwas daga abin da kuka bari bayan (an zartar da wasiyya da kuka yi, ko wani bashi da ke kanku…”.

A fiarshe, ina tukuicin salati ga Manzonmu Annabi Muhammadu da iyalansa, tare da fatan Allah ya fiara yarda da sahabbansa da duk wanda ya bi bayansu da kyautatawa har zuwa tashin kiyama. Ina kuma rofion Allah ya mini dalilin samun Aljannar Firdausi, amin. Ya Allah ka saka wa duk wanda ya ba da gudunmawarsa game da kammaluwar wannan littafi da alheri,amin.

Ɗan’ uwan ku a Musulunci,

**Abubakar Abbas**

**Hotoron Arewa**

**Kukar Dillalai, Kano**.

**1434H=2013M.**